# SŨRATUT TAKÃTHUR سُورَةُ التَّكَاثُرِ

Tana bayãnin hana alfahari, sabõda dũkiya ko dangi.

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Alfahari da yawan dũkiya da dangi ya shagaltar da ku (daga ibada mai amfaninku).

*2.* Har kuka ziyarci kaburbura.

*3.* A'aha! (Nan gaba) zã ku sani.

*4.* Sa'an nan, tabbas, zã ku sani.

*5.* Haƙĩƙa, da kuna da sani, sani na yaƙĩni.

*6.* Lalle ne da kuna ganin Jahĩm.

*7.* Sa'an nan lalle ne za ku gan ta, da idanu, bayyane.

*8.* Sa'an nan lalle ne za a tambaye ku, a rãnar nan, lãbãrin ni'imar (da aka yi muku).

أَلْهَىٰكُمُ ٱلتَّكَاثُرُ ①

حَتَّىٰ زُرْتُمُ ٱلْمَقَابِرَ ②

كَلَّا سَوْفَ تَعْلَمُونَ ③

ثُمَّ كَلَّا سَوْفَ تَعْلَمُونَ ④

كَلَّا لَوْ تَعْلَمُونَ عِلْمَ ٱلْيَقِينِ ⑤

لَتَرَوُنَّ ٱلْجَحِيمَ ⑥

ثُمَّ لَتَرَوُنَّهَا عَيْنَ ٱلْيَقِينِ ⑦

ثُمَّ لَتُسْـَٔلُنَّ يَوْمَئِذٍ عَنِ ٱلنَّعِيمِ ⑧